# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tudun mun tsira – Mai bayani a kan ’yan Afirka da ke yin ƙaura zuwa Turai
## Kashi na farko: Fata na gari lamiri

Wadda ta rubuta: Chrispin Mwakideu
Wanda ya fassara: Ɗanlami Bala Gwammaja
Wadda ta tace: Halima C. Schmaling

**’Yan Wasa:**

Lami: ’yar shekara 20
Magaji: ɗan shekara 22
Faisal: ɗan shekara 19
Suleman: ɗan shekara 19
Malam Talle: ɗan shekara 60
Matar Malam Talle: ’yar shekara 55

**Mai gabatarwa:**

Masu saurarenmu, barkanmu da sake saduwa a cikin shirinmu na “Ji Ka Karu”. A yau za mu gabatar muku da wani sabon wasan kwaikwaiyo ne mai taken “Tudun mun tsira – Mai bayani a kan ƙaurar ’yan Afrika zuwa Turai”. Tarihi dai ya nuna cewa mutane sun sha yin ƙaura zuwa wasu garuruwan don neman inganta rayuwarsu. A zancen da ake yi yanzu, da wuya a samu wata rana da ba za a samu labarin isowar ’yan gudun hijira ba zuwa ƙasashen Turai daga nahiyar Afirka da kuma sauran nahiyoyi. Yawancin waɗannan mutane kan yi kasada da komai, har ma da rayuwarsu, don dai su samu yin ƙaura zuwa “Tudun-mun-tsira”. Sai dai kuma, ba wai dukkansu ba ne ke zuwa ƙasashen Turai ta ɓarauniyar hanya, waɗansunsu kan samu takardun izinin zama a waɗannan ƙasashe. To, ko wane dalili ne yakan sa mutanen Afrika suke ficewa daga nahiyar tasu? Kuma ko me za su fuskanta idan sun isa ƙasashen Turan? Domin jin amsoshin waɗannan tambayoyi, da ma dai sauran batutuwa, sai ku kasance da mu don ku saurari kashin farko na shirinmu mai taken “Fata na gari lamiri”.

A cikin wannan shiri, za ku haɗu da waɗansu matasa da suka fito daga sassa dabam-dabam na nahiyar Afirka. Akwai Magaji da Lami waɗanda suke da zama a can kudancin Sahara. Waɗannan matasa biyu sun kasance abokan juna tun suna ƙanana. Yanzu ga shi sun zama matasa, kana kuma dangantakar tasu ta daɗa haɓaka. Kuma ba su daɗe da kammala karatunsu na jami’a ba. Shi dai Magaji so yake ya zama magidanci, amma kuma iyayen Lami ba wannan ne a gabansu ba. To, ko ta yaya Magaji da Lami za su fuskanci wannan matsala? Sai ku biyo mu don ku ji irin hirar da waɗannan masoya ke yi, a yayin da suka haɗu a wani gidan cin abinci da ke cikin gari.

**Fitowa ta 1: Magaji da Lami a gidan cin abinci**

**Magaji:** Lami, wai me kike saƙawa a ranki ne? Na ga kin shiga kogin tunanin.

**Lami:** Wallahi Magaji, ni... ni na ma rasa ta yadda zan gaya maka

labarin da na zo da shi.

**Magaji:** Mmmh… To tsaya, labari mai daɗi ne ko mara daɗi? Ni na ga duk hankalinki ya tashi. Ya kamata ki saki jikinki. Kin manta ne, kwanan nan muka kammala karatunmu, kuma ga shi sakamakonmu ya yi kyau. Kin san fa ba za mu samu wata matsala ba idan muka je neman aiki.

**Lami:** Ni fa ƙasar nan zan bari.

**Magaji:** Me kike cewa, Lami? Wai don Allah me kike cewa?

**Lami:** Magaji, ka kwantar da hankalinka mana. Cewa na yi zan tafi Turai don ci gaba da karatuna.

**Magaji:** Tsaya mana Lami, ai alƙawari bai ce haka ba! Don Allah kar ki tafi ko'ina. Kin san za ki iya ci gaba da karatunki ma a nan ƙasar.

**Lami:** To ai bakin alƙalami ya riga ya bushe, Magaji. Ni yanzu ba ni da ikon canza abin da iyayena suka zaɓa min. Sun riga sun gamsu cewa ci gaba da karatuna a Turai zai ba ni damar samun aiki cikin sauƙi.

**Magaji:** To yanzu shi ke nan ni? Haba Lami, kin san ni mai ƙaunarki ne. Yanzu so kike na manta da duk irin soyayyar da muka yi da ke?

**Lami:** Kai kuwa Magaji me ya sa kake irin wannan magana haka! Kai kana ji idan na tafi shi ke nan har abada ba zan dawo ba? Magana ce fa kawai ta shekara uku. Kuma kai kanka ka san yadda nake son mu kasance tare.

**Magaji:** Shekara uku fa kike cewa! Haba Lami, nan da shekara uku ai sai buzuna.

**Lami:** Don Allah Magaji, ka daina irin wannan magana mara daɗi. Kai kanka ka san hakan shi ne mafi alheri a gare mu duka. Kuma za fa mu dinga haɗuwa ta *Facebook*, sannan kuma za mu dinga hira ta intanet. Wallahi gani za ka yi kamar ga ni ga ka. Kuma da yake lokaci tafiya yake cikin sauri, kafin ma ka ankara, sai ka ga har ma na gama na dawo mun kasance tare.

**Magaji:** To ni yanzu wane tabbaci nake da shi. Sai dai fa idan…

**Lami:** Idan fa me?

**Magaji:** Sai dai fa idan kin yi min alƙawarin za ki aure ni idan kin dawo.

**Lami:** Gaskiya Magaji, ba ka yi min adalci ba idan ka ce sai na ɗaukar maka irin wannan alƙawarin.

**Magaji:** Ai kuwa in dai son da kike yi min na gaske ne, sai kin ɗaukar min wannan alƙawari. Haka ne kawai zai sa na jure idan kika yi tafiyarki kika bar ni.

**Lami:** Ni dai gaskiya Magaji… ni ba zan iya ɗaukar irin wannan alƙawarin ba, sai dai ka yi haƙuri. Idan na yi hakan zan ɗaure kaina ne, kuma ka ga a gidanmu kowa da ni yake ji...

**Magaji:** Haba Lami, bai kamata ki yi mini haka ba. In ba ke ba ni! Ke Lami! Kai! Na shiga uku!

**Mai ba da labari:**
To, ko me Lami za ta yi bayan da ta tashi a fusace daga wurin da suke cin abinci, ita da Magaji? Sai ku biyo mu don ku ji abin da zai wakana. Amma kafin nan, bari mu yi ɗan tattaki kaɗan zuwa arewacin Afirka inda za mu haɗu da wani matashi maraya mai suna Faisal wanda tuni iyayensa suka mutu, suka bar shi. Kuma a yanzu haka ga shi can shi da abokinsa Suleman, wanda shi ma matashi ne ɗan Afirka ta Arewa, kuma ya fito ne daga gidan masunta. Dukkaninsu dai ba su da aikin yi, kuma abu ɗaya kawai suka ƙwallafa wa ransu, wato yadda za su kai ga zuwa Turai.

**Fitowa ta 2: Faisal da Suleman na dawowa daga sallah**

**Suleman:** Faisal, tunanin me kake yi haka ne?

**Faisal:** Huh? Kai ba komai, ba wani abu ba ne, kawai dai ina…

**Suleman:** A'a, tabbas akwai wani abu! Ga shi nan na lura kwana biyu ba ka yawan magana. Wai me ke faruwa ne, Faisal?

**Faisal:** Wallahi Suleman, ba wani abu. Kawai dai wani lokaci nakan tambayi kaina, wai yaushe za mu taɓa samun zaman lafiya a wannan ƙasa tamu? Dubi dai yadda ƙiyayya da gaba da ɗaukar fansa suka yi ƙamari. Ka ga fa Suleman, ta sanadiyyar haka na rasa iyayena. Wallahi ni duk abin ya ishe ni. Kamata ya yi kawai mu haura…

**Suleman:** Mu haura ƙasashen waje ko? Wato kai dai har yanzu kana nan a kan bakanka ko? Faisal na fa lura cewa kana jin daɗin ka dinga mafarkin zuwa Turai. Ni ma ina yi, amma ya kamata mu sani cewa a nan ƙasar Allah Ya nufe mu da zama.

**Faisal:** Ina! Ta ina mutum zai yi rayuwarsa a wannan ƙasar? Ai mutane na Turai, kuma a can ake rayuwa.

**Suleman:** Me kake cewa? Ba rayuwa muke yi a nan ba? To Faisal, yanzu mutuwa ka yi? Ni gani nake a cikin matattun ma kai a raye kake!

**Faisal:** Suleman, ba cewa na yi mun mutu ba, amma ka sani ba rayuwa muke ba. Ga mu nan dai kawai.

**Suleman:** Ga mu nan dai kawai?

**Faisal:** Kwarai kuwa. A kullum fa sai mun yi fafutakar abin da za mu ci. Amma daga yadda nake samun labarin, Turai ta nunka nan sau ɗari. Gaskiya rayuwar can ta fi ta nan, nesa ba kusa ba ma. Idan har mutum zai samu damar tsallakawa zuwa Turai, a nan zai san yana rayuwa. Zo mu je bakin gaɓa don mu dinga hango hasken Turai.

**Suleman:** Kai, Faisal, zancenka ke nan dai kullum, 'mu je mu ga hasken Turai'. To, mu je!

**Faisal:** Ka ga kuwa Suleman, wata rana sai na tsallaka ƙetaren can, a lokacin ne zan san a raye nake.

**Mai ba da labari:**
To fa, wannan shi ne irin mafarkin da Faisal da Suleman da ma sauran matasan nahiyar Afirka ke yi na tsallakawa zuwa Turai. To, a wannan rana dai da yammaci a can gidan su Lami, ga iyayenta, wato Malam Talle da matarsa can sun kasa kannewa saboda wata murna da suke yi.

**Fitowa ta 3: Da yammaci, a gidan su Lami**

**Malam Talle:** Madalla! Lami wai kin tattauna da Magaji a kan maganar ci gaba da karatunki a Turai kuwa?

**Matar M. Talle:** Yauwa, ni ma da ma abin da nake so na tambaye ki ke nan. Na san yau kun fita cin abinci, ko ba haka ba ne?

**Lami:** Mama, yaya aka yi kika sani, ko kin biyo mu ne?

**Matar M. Talle:** Mmm… ƙwarai kuwa, a shafin *Facebook* ba?! Bayan kowa na ganinku. Ai abin da Magaji ya rubuta dab da lokacin shi ne: "Don Allah kar a dame ni, na fita cin abinci da rabin raina. "

**Malam Talle:** Kai! Wannan zamani ya lalace. Wai a ce mutane yanzu ba za su iya ɓoye sirrinsu ba!

**Lami:** Ni gaskiya ba a yi mana adalci ba.

**Malam Talle:** Ke Lami! Me kike cewa?

**Lami:** Ta yadda za ku cilla ni wata uwar duniya ba tare da kun yi tunanin irin abin da zan tafi na bari a baya ba.

**Matar M. Talle:** Wace uwa za ki bari a wannan ƙasar tamu in ban da tsananin talauci da ɓacin rai?

**Malam Talle:** Tsaya Maman Lami, ya kamata mu ba ta dama ta yi bayanin abin da take nufi! Ina jinki Lami, na ji kina cewa…?

**Lami:** Baba, Mama, na san kuna sona da alheri, kuma wallahi na

yaba da abin da kuka yi min. Sai dai kuma wannan tafiyar da zan yi zuwa ƙasar waje, ta ɓata tsakanina da Magaji.

**Malam Talle:** Ta wace hanya ke nan Lami? Ko ya yi miki barazanar zai rabu da ke ne bayan da kika gaya masa abin alherin da ya same ki?

**Lami:** Da ma wannan ita ce matsalar da nake gudu. Ku a wajenku wannan abin alheri ne, amma a gun wasu ba haka ba ne. Magaji ba barazana zai bar ni ya yi ba, cewa ya yi na aure shi.

**Matar M. Talle:** Lallai wannan shi ne cikakken ɗan Afirka.

**Malam Talle:** Wai ke Maman Lami, mantawa kike yi ne cewa ni ma ɗan Afirka ne. Na san dai zamani ya canza, don haka ni ma nake son Lami ta yi karatun aikin lauya. Kuma...

**Lami:** Amma Baba, kun san zan iya ci gaba da karatuna a ƙasar nan, me ya sa za a ce sai an tura ni wata uwar duniya? Wato fa yanzu sai na shafe shekaru uku ke nan kafin na sa Magaji a idona.

**Matar M. Talle:** Ke Lami, tsaya ki ji! Ni da babanki mun sha wahala domin mu tabbatar da cewa kin ƙaro karatu a Turai. Mun kashe duk kuɗin da muka ajiye domin mu biya miki ki tafi karatu. A ce wai yanzu kina kwatanta abin da muka yi miki da wani wai shi Magaji, ba ma ki gode mana da abin da muka yi miki ba? Kuma wannan ma ai rashin ladabi ne ga iyayenki.

**Malam Talle:** Lami, abin da babarki take faɗa gaskiya ne. Ki sani fa cewa damar da za ki samu a can babu irinta a nan ƙasar. Amma idan Allah Ya sa kika mai da hankali kika yi karatu, za ki ga

canji a rayuwarki. Kin ga dai za ki samu aiki, kuma za ki samu damammaki da yawa, kuma kuɗi za su dinga shigo miki. Sannan kua wataƙila wata rana ki ji can ɗin ma ta fi miki. Ya kamata ʼyata, ki dai sake tunani, rayuwar nan dai taki ce.

**Lami:** To shi kuma Magajin fa? Ya ce in yi masa alƙawarin zan aure shi idan na dawo. To ni yanzu yaya zan yi?

**Matar M. Talle:** Ba sai ki ce masa za ki amsa masa ba idan kin dawo. Kuma ki ce masa wannan maganar tsakaninku ne kawai, ba sai ya tallata ta a *Facebook* ba.

**Malam Talle:** Ni wallahi ban san abin da ya sa ku matasa kuka nace wa *Facebook* ɗin nn ba. Ke Lami, wai don Allah ba kya ganin cewa kin girma ne? Ya kamata komai za ki yi, ki dinga yi kamar na waɗanda suka mallaki hankalinsu.

**Mai gabatarwa:**

To masu sauraro, da waɗannan kalamai na Malam Talle muka zo ƙarshen wannan kashi na farko a shirinmu na "Ji Ka Karu" wanda ke bayani a kan ƙaurar da matasa ke yi zuwa ƙasashen Turai. Ko me Lami za ta yi nan gaba game da masoyinta Magaji? Shin wai gaskiya ne cewa matasan Afirka ba su da wata dama a wannan nahiyar?

Sai ku aiko mana da ra'ayoyinku ta cikin shafin Facebook ta adireshi facebook.com/dw.lbe. Kafin nan, sai mu ce ku huta lafiya**.**